Takardar Bayanai Masu Muhimmanci

# Aiki tare da Wa'yanda suka Tsira daga Ci da gumi Cin zarafi da Tursasawa ta Hanyar Jima'i (SEAH)

Wannan takardar bayanai masu muhimmanci abin dubawa ce don fahimtar halayya masu kyau a lokacin aiki tare da waɗanda suka tsira daga SEAH don wallafa ka'idoji.[1] Yana ba da jerin muhimman abubuwa da tambayoyi waɗanda ya kamata ƙungiyoyi su tambaya a lokacin aiki tare da waɗanda suka tsira.

Masu tsirar na iya ba da gudummawar su mai mahimmanci a lokacin shirya ka'idodi akan amfani da dama, cin zarafi da tursasawa ta fuskar jima'i (SEAH). Duk da haka, sanya hannu mai ma'ana ya ƙunshi masu tsara manufofin aiki yadda ya dace da kuma ɗaukar nauyi don tabbatar da cewa an saurari muryar waɗanda suka tsira ba tare da ƙara cutar da su ba.

## Meyasa za'a yi aiki tare da wa'yanda suka tsira?

- ✓ Kungiyoyi nada alhakin ɗaukan ra'ayoyi da abubuwa da masu tsira suka fuskanta da mahimmanci
- ✓ Masu tsira kwararru ne don abubuwan da suka fuskanta kuma sun fi sanin fiye da kowa abubuwan dake aiki da wanda basa yi
- ✓ Sanya shi cikin ka'ida da canji na iya taimakawa wa'yanda suka tsira da warwarewa kuma su ji an darajanta su
- ✓ Aiki tare da wa'yanda suka tsira na iya tabbatar cewa aikin yana da mahimmanci kuma zai yi tasiri
- ✓ Ma'aikata da Kungiyoyi zasu fi taka rawar su idan sun fahimci SEAH daga ra'ayin wanda suka tsira

## Lokain da ba za'a yi aiki da wa'yanda suka tsira ba

- ✗ Idan har yanzu masu tsirar suna cikin hatsari kai tsaye daga mai (ko masu) aikata laifin
- ✗ Idan ƙungiyarku ba su da wata ka'ida mai kyau da hanyoyin kiyaye da kare waɗanda suka tsira da masu fallasa a duk lokacin aiki da bayan aiki tare da su
- ✗ Idan aiki da su zai jawo musu illa ko sa su cikin hatsari duk daga masu aikata laifuka, al'umma ko gwamnatoci (misali fansa don yin magana kamar daurin kurkuku ko rasa matsayin Shari'a)
- ✗ Idan aiki da su don moriyar ƙungiyar ne kawai ba wai ana la'akari da mai tsirar ba
- ✗ Idan ƙungiyarku ba su da niyyar ƙokarin aiwatar da shawarwarin da waɗanda suka tsira suka bayar

Ma'anonin masu Amfani:

**Hanya mai la'akari da wanda ya tsira**: Tabbatar cewa matakan kariya da daukar mataki babu nuna banbanci kuma akwai girmamawa da ba da hakkoki, buƙatu da ra'ayoyin waɗanda suka tsira mahimmanci, har da gungun mutane da suka fi shiga cikin hatsari ko kuma ana nufar su musamman don SEAH.[2]

**Hanyar da mai tsirar ke jagoranta**: Wata hanyar wadda ke bawa masu tsira kayan aiki da karfafawa don jagorantar rayuwarsu da kuma gwagwarmaya akan kowane nau'in cin zarafi da/ko ke cutarwa da suka sha fama da shi kuma sun shawo kansa.[3]

**Hanyar da ake la'akari da yanayin rudani**: Wata hanyar da take la'akari da tasirin rudani na gama gari kuma su fahimci hanyoyi mai yiwuwa don warwarewa. Wannan ya hada da gano alamun rudanin; haɗa ilimi game da rudani gabaki daya a cikin ka'idoji, hanyoyin aiki da ɗabi'u da kuma aiki tukuru da manufar hana ƙara tsoratar da su.[4]

Teburin da ke kasa na jagorantar ƙungiyoyi su shirya yadda za su yi aiki tare da waɗanda suka tsira. Wannan jerin ba iyakarsa kenan ba amma ana so a gabatar da tunani game da abin da aiki tare da waɗanda suka tsira ya ƙunsa.

Augusta 2020

## Samar da muhalli mai aminci kuma mai saukin samu



**Tabbatar an ƙafa matakan kiyayewa ga waɗanda suka tsira da masu fallasa.** Shin ka'idoji da hanyoyin kariyarku an sabunta su kuma har yanzu sun dace? Shin kuna da wata hanya don goyon bayan waɗanda suka tsira idan sun bayyana abun da ya faru a lokacin aiki da su ko bayan nan?

**Tabbatar an aiwatar da shirin tsaro.** Shin kun aiwatar da binciken hatsarorin aiki tare dasu? Shin kun yi aiki tare da wa'yanda suka tsira da ma'aikata/masu gudanarwa don haɗa shirin tsaro a lokacin da bayan aiki tare da su?

**Tabbatar cewa akwai tallafi don waɗanda suka tsira idan wani abu ya shafe su a lokacin tattaunawar**. Waɗanne hidimomi ake buƙata? Shin su waye kuke buƙatar haɗa kai da su? Shin kun yi la'akari da matakai na musamman don yara? Shin kun yi la'akari akan yadda za'a biya kuɗin hidimomi?

**Tabbatar da muhalli mai sauki kuma ba'a ware kowa ba.** Shin yaya za ku shigar da waɗanda suka tsira daga yankuna daban-daban ko kabila daban-daban? Yaya za ku taimakawa waɗanda suka tsira da sufuri zuwa wajen taron? Yaya za ku tallafawa iyaye da kulawa da yara, mutane masu nakasa ko sauran ƙungiyoyi don aikin?

**Tabbatar da sirri da boye bayanan kai.** Shin akwai yiwuwa a gano waɗanda suka tsira a lokacin halartar taron? Shin kuna sirranta kowane aiki da kuma cire duk abubuwa da zai sa a gano ko waye ne daga labaransu?

## Aiki tare da su a hankali, da fahimta da kuma tunani



**Ya kamata tsarin aiki ya zama jagora da tsaran wa'yanda suka tsira** Shin kun yi la'akari da yadda wa'yanda suka tsira zasu yi jagora kuma su taka rawa wajen tsara aikin da shirya ka'idodi ta hanyar da ba zai jawo ƙarin illa ba? Shin kun tambayi waɗanda suka tsira hanyoyin da za su yi musu aiki?

**Tabbatar an karbi izini na duk kowane taro da hotuna, maganganu ko aikin rubutu da aka yi amfani da shi.** Shin kun yi bayani me aikin ya ƙunsa da kuma bayyana menene bada izini ta wata hanyar da mai tsirar zai fahimta? Shin kun yi bayani cewa za su iya dakatar da tattaunawar a kowane lokaci? Shin kun yi bayani yadda za'a yi amfani da kowane hotuna, maganganu ko rubutaccen aiki da kuma su waye za su gani? Shin za'a wallafa kowane aikin a yanar gizo ko wani takardar jama'a da aka buga?

**Ku fayyace, zama masu gaskiya kuma nuna abin da zai yiwu game da abubuwan da ake tsammani.** Shin kana nuna abin da zai yiwu game da abubuwan da kuke iya samun nasara akai don kayayyaki da kuke da shi da lokaci? Shin kun fayyace abin da ake tsammani daga aiki tare? Shin masu tsirar sun fayyace matsayinku da kowane cikas da za a samu? Shin kun ce za ku kira, tura sako ko tura bayani? Idan haka ne, ku tabbatar kun yi.

**Ya kamata sadarwar ta zama a bayyane kuma a nuna abokantaka kafin da bayan aiwatarwa.** Shin sadarwar tare da waɗanda suka tsira na sa su ji kwanciyar hankali? Shin kun yi bayanin tsarin, menene zai faru da kuma bibiyar da ake buƙata? Shin muryarka da motsin jikinka sun nuna abota? Shin kun yi tunani game da naku ra'ayin da son kai da kuma yadda zai iya shafar sadarwa tare da mutane?

**Bada zaɓi daban-daban don waɗanda suka tsira su iya zaɓin yadda suke son hulɗar.** Shin kun yi la'akari da hanyoyi daban-daban don aiki tare da waɗanda suka tsira (a rubuce, sauti, zane, da sauransu)? Shin mai tsirar ya fahimci zaɓin daban-daban da rawar da za su taka ko ra'ayin da suka kasance da shi?

## Samar da kayayyaki da hanyoyin canzawa a sauwake



**Tabbatar kun yi abin da zai yiwu game da ɗaukar ma'aikata da lokacin aiki tare da waɗanda suka tsira.** Shin kun samu isassun kwararrun ma'aikata don tallafawa aikin, musamman a lokacin aiki tare da yara da nakasassun mutane? Shin kun yi wani shiri daban don kowane canji da za'a iya samu wanda ba'a yi tsammani ba? Misali idan mai tsirar ya janye daga baya, amma kuma yana son hulda? Shin kuna iya kara haɗa wani taron?

**Yi la'akari da farashin taron.** Shin za ku ba da abinci a lokacin taron? Shin ana buƙatar biyan kuɗin wurin da za'a yi taron? Shin kuna buƙatar filin rarrabawa zuwa kananan gungu don hutu ko tattaunawa daban? Shin kuna buƙatar masu fassara?

**Biyan kuɗi don ƙwarewar masu tsirar.** Shin za ku bada kuɗi don lokacin da waɗanda suka tsira suka bayar? Shin za ku mai da musu kuɗaɗen da suka kashe na sufuri da masauki (wata kila masu tsirar zasu buƙaci wannan don su samu zuwa wurin taron)? Shin za ku biya kuɗin kulawa da yara ko kuma kula da yaran?

[1] An sauya wannan takardar shawara daga wani rahoto da aka rubuta don Cibiyar Kayayyaki da Tallafi: RSH (2020) Dabi'u mafi kyau don shigar da wa'yanda suka tsira daga cutarwa, cin zarafi da barazana ta fuskar jima'i (SEAH).https://safeguardingsupporthub.org/best-practice-engaging-survivors-sexual-exploitation-abuse-and-sexual-harassment

[2] Boezio, G., n.d. Landmark Yarjejeniyar Majalisar Tsaro na UN 2467 (2019) karfafa adalci da ɗaukan alhaki da kira ga wani hanya mai la'akari da wa'yanda suka tsira a hana da tallafawa rikici mai alaka da tashin hankali ta hanyar jima'i, 29 Afrilu 2019. Majalisar Dinkin Duniya https://slavefreetoday.org/journal_of_modern_slavery/v2i1a2_Rise_Unite_Support_Doing_No_Harm_in_the_AntiTrafficking_Movement_countryman_roswurm.pdf

[3] Countryman-Roswurm, K. (2015). Tashi, haɗa kai, goyi baya: Kar a "cutar" a gwagwarmayar nuna gaba da fataucin mutane. Slavery Today Journal: A Multidisciplinary Journal of Human Trafficking Solutions, 2, 1. URL https://slavefreetoday.org/journal_of_modern_slavery/v2i1a2_Rise_Unite_Support_Doing_No_Harm_in_the_AntiTrafficking_Movement_countryman_roswurm.pdf

[4] Mentalhealth.org (2015) Hanya mai La'akari da Rudani da Taimako don Rudani na Musamman. Accessed 04.08.20 URL https://www.mentalhealth.org/get-help/trauma#:~:text=Recognizes%20the%20signs%20and%20symptoms,actively%20resist%20re%2Dtraumatization.%22